

# Samar da kuɗi wa ƙananun Kasuwancin ku
2022-2023

**New York Immigration Coalition**
nyic.org

TEBURIN ABUBUWAN DA SUKE CIKI


## I. GABATARWA

Yanda Za ayi Amfani da Wannan Jagora 1

## II. BASHIN KASUWANCI

Fahimtar Bashin Kasuwanci 2
Samar da Bashin Kasuwanci 3

## III. ZAƁUƁƁUKAN SAMAR DA KUƊI

Samarwar Kashin Kai 4
*Abokai da Iyali* 5
*Samarwan taron jama'a* 6
*Samarwan dandalin taron jama'a* 7
Tallafi 8
Bashi 9
*Hanyoyin da za a Cika neman Bashi* 10
*Cika Bashin kananun kasuwanci na Gaba-daya* 11
*Jerin abubuwan dubawa*

## IV. ALBARKATUN

Al'ummar Jahar New York
Ma'aikatar Cika an Kuɗi 12

## Yadda Za Ayi Amfani da wannan Taimako

Muhimmin al'amari na ƙaddamarwa ko haɓaka ƙaramar kasuwanci shine fahimtar zaɓuɓɓukan samar da kuɗi waɗanda ke akwai don taimaka muku biyan bukatun kasuwancin ku. Baƙi- su ne suka mallaki kashi 33.8% na kananun kasuwancin mallakar mazauna Jihar New York kuma wannan shine burinmu na haɗa wannan al'ummar tare da bayanai da suka dace da albarkatun da aka ware don taimaka wa baƙi wanda suka mallaki ƙananun kasuwanci da 'yan kasuwa.

Wannan jagorar za ta zama abun da baƙi ƙananun yan kasuwa zasu yi amfani a matsayin gabatarwa wajen samar da bashin kuɗi, bayyani na zaɓuɓɓukan samar da kuɗi, da kuma jigon aikace-aikacen ba da bashi na gaba ɗaya. Zaɓuɓɓukan samar da kuɗin da kuka zaɓa zai yi tasiri akan tsarin kasuwancin ku da makomar kuɗin ku. Yana da muhimmanci ku yi la'akari da tayaya samar da kuɗi zai taimaka muku wajen cimma burin kasuwancin ku da kuma biya muku buƙatun ku na kuɗi.

Wannan jagorar bai rufe buƙatu kamar lasisi ko izini, ya kamata a yi amfani da wannan jagorar mazaunin ra'ayoyin samar da kuɗi kasuwanci na gaba ɗaya. Dan Allah a duba jagoran Kananan Kasuwancin Baƙi a **https://www.nyic.org/immigrant-small-business-guide/** don ƙarin bayanai

## Fahimtar Bashin Kasuwanci

Kafin ku yanke shawarar samar da kuɗi wa kasuwancin ku. **Bashin Kuɗi**, kamar bashin kuɗin amfanin kai, kamata yayi masu bada bashi kuɗin su ba zai salwanta in suka ba ku bashin.Yana taimakawa masu bada bashin auna cancantar a cin bashi, ko gwargwadon yadda kasuwanci ya dace don samun tallafin kuɗi. Masu bada bashin suna gane hakan ne idan suka yi dubi tarihin hada haɗar kuɗi da kuma iya biyan bashin ku.

Bashin kasuwanci yakamata a a buɗe shi da sunan kasuwancin. Wannan zai tabbatar da bashin da an banbanta bashi da aka ciki don kasuwanci da na amfann kai. Wannan yana da muhimmanci saboda:

- Rarraba hanyoyin bashin ku yakan tsare muku bashin ku daga kowane mummunan tasiri da kasuwancin ku zai iya fuskanta
- Kasuwancin ku na iya fara haɓaka bashin da haɓaka damar ku na samun bashi da sauran hanyoyin samun kuɗi
- Kuna iya gano mafi kyawun hanyar kashe kuɗaɗen kasuwanci don haraji

## Tarihin Bashi

Tarihin bashi yana da tasiri wajen samu damammaki samar da kuɗi, farashin inshora, kuma yana taimakawa abokan hulɗar kasuwanci, masu kaya, da masu siyarwa wajen yanke shawarar ko zasu yi kasuwanci da ku. Tarihin bashi yana bada dama wa abokan hulɗan da masu bada bashin sanin ko kasuwancin ku zai girma kuma zai zama me duba.

Masu bada bashi sukan yi amfani da tarihin bashi don ganowa shin yakamata su bawa kasuwancin ku bashi. Duk ka tarihin bashin amfanin kai da na kasuwanci a na la'akari da su wajen tantancewa ko kun cancanci a baku bashi.

Lokacin da hukumomin bayar da rahoto bashi kamar su Experian, Equifax, da Dun & Bradstreet su ka kimanta bashi ku akasari sukan yi amfani da jerin abubuwa masu **zuwa**:

| | | |
|---|---|---|
| Shekarun da ku kayi a Kasuwanci | Layikan bashin da akayi amfani dashi a watanni 9 da suka wuce | Layikan bashin da aka buɗe a watanni 6 da suka wuce |
| Saunawa aka yi jinkirin biya | Girman masana'anta da kamfani | Tarihin biya na watanni 12 da suka wuce |

| Yadda za a Samar da Bashin Kasuwanci | |
|---|---|
| **Zaɓi Tsarin Kasuwanci** | • Duk tsarin kasuwanci suna ware kasuwancin ku daga bashin amfanin kai sai dai tsarin kasuwancin mallakin kai<br><br>• Zaku iya kara koyan tsarin kasuwanci a nan: https://www.nyic.org/immigrant-small-business-guide/ |
| **Sami Lambar Shaidan Ma'aikata (EIN)** | • Shi EIN ana iya sanin sa a matsayin Lambar Shaidan Harajin Tarayya. Ana yin amfani da shi wajen gane muhallin kasuwanci. Kasuwancin yana buƙatar EIN don ku iya shigar da haraji, buɗe asusun banki na kasuwanci, da kuma neman bashin kasuwanci, dama, da kuma lasisi<br><br>• Zaku iya neman EIN ta amfani da wannan kayan aikin IRS: https://www.irs.gov/ein |
| **Buɗe Asusun Kasuwanci** | Buɗe asusun kasuwanci yana da amfani don ware kashe kashen kuɗin don amfanin kai da kuma kasuwanci. Banki zasu iya tsaya muku wajen ciki neman bashi |
| **Samar da Bashi tare da Masu Siyarwa/Masu kaya** | Siyan kayayyaki, sinadarai, ko wasu kayan daga masu siyarwa da masu kaya yana zai taimaka wajen haɓaka samun bashin ku |


## Samarwar Kashin Kai

**Samarwar Kashin Kai**, ko cigaban kai, yana nufin in ka samar da kuɗin kasuwancin ka da dukiyar ka. Ba a kowane lokaci bane sabin yan kasuwa suke samun kuɗin da za su samar a kasuwancin su, don haka dole ne su yi la'akari da wasu kadarorin kamar hannun jari ko zuba jari, katin kai na bashi ko cin bashi.

Samarwar Kashin Kai yana bawa yan kasuwa damar yanke shawarar da kuma riƙe kashi 100% daga abun da suka siyar da kuma hannun jarin su. Yana da mahimmanci mu tuna cewa samar da kuɗin kai mai mallakar kasuwanci dole ne ya ɗauki duk haɗari da alhakin da ke tattare da kasuwancin.

Ayayin samar da kuɗin kai kuna son tabbatar da kasuwancin ku yana da samar da riba da wuri-wuri. Kuna so ku sami damar sake juya kuɗin da kuka saka a kasuwancin.

A maimakon juyawa ga masu saka hannun jarin ko bankuna, Masu ciga ba sukan juyawa zuwa ga iyalansu da abokan su ne a ko da yaushe don taimako ko a tara musu.



## Abokai da iyalai

Abokai da iyalai a ko da yaushe sune farkon hanyar samun taimako wa yan ƙananan yan kasuwa saboda alaƙa da kuma yarda da burin ku da kuma iyawar ku.

Saboda shingen da wasu 'yan kasuwa ke fuskanta lokacin neman bashi da samun masu zuba hannun jari, tallafin kuɗi daga abokai da iyali galibi shine babban tushe. Suna iya tallafawa kasuwancin ku ta hanyar kyauta, bashi, ko saka hannun jari. Haka zalika za su iya ba ku kuɗi ba tare da sun sa muku wani doka mai tsauri ba ko bashi wanda ke ba da jadawalin biyan kuɗi mafi sauƙi.

A ko da yaushe ku kasance masu gaskiya wajen hadaruruka da alhakin da ke tattare da kasuwancin ku kuma ku ƙirƙiri bayyanannu sharudda lokacin karɓar rancen kuɗi. Yi la'akari da waɗannan mahimman matakai yayin neman tallafi daga abokai da iyalai:

| | |
|---|---|
| **Zama Takamaimai** | • Nemi takamaiman adadin kuɗi don takamaiman manufa |
| **Kasance Mai Gaskiya** | • Menene jarin ku?<br>• Menene himmar ku wajen cimma manufofin ku?<br>• Manene haduran da suke tattare da shi? |
| **Kun Rubuta Yarjejeniyoyi waɗanda ke Bayyana Sharuɗɗan Bashin** | • Adadin Bashin tare da adadin riban<br>• Dalilin Bashin<br>• Sharuɗɗan biyan kuɗi - a dunƙule ne ko biyan kuɗi na yau da kullun; adadin kowane biya<br>• Jadawalin lokacin biyan kuɗi wanda yake bayyana lokacin da aka fara biyan kuɗi da sannan nen lokacin da za a gama biya<br>• Sakamakon rashin biya |

## Samarwan taron jama'a

Samarwan taron jama'a shine lokacin da kuka tara kuɗi don ayyukan kasuwanci da kashe kuɗi daga wajen al'umma. Wanan yana faruwa ne ta hanyar dandamalin yanar gizo.

Akwai manyan nau'ika guda biyu waɗanda zaku iya amfani da su wajen samar ma ƙaramin kasuwanci ku kuɗi ta hanyar taron jama'a:

- Taimakon Samar da Kuɗi - tara kuɗi daga mutane don tallafawa kasuwancin ku ba tare da karɓar komai ba. Wannan shine mai ƙarancin haɗari, hanyar samun riba mai girma ga ƙananun kasuwanci
- Samar da kuɗi don lada - masu ba da gudummawa suna karɓar dan lada, kaya, ko ayyuka don musayar gudummawarsu da suka bayar. Kamar misali, idan kuna buƙatar siyan sabon tanda don yin burodin ku, kuna iya ba su tikitin rangwamen kek da zarar sun bada gudummawa su.

## Abun Mai amfani da Mara amfani a samar da Kuɗin daga Taron jama'a

Dandalin samar kuɗin taron jama'a ya samar da amfani masu yawa kamar su kara sanayyar kayan, taimakawa wajen samar da tushen abokan ciniki sanan rage haɗari kuɗin kashin kan ku. Hakanan zaku iya bincika kamfanoni masu irin wannan kamfen na samar da kuɗin taron jama'a don ganin irin abubuwan ƙarfafa guiwa da suke bayarwa da kuma sani ko sun yi ci nasara.

Duk da haka, yi nasara tare da samar da kuɗin taron jama'a ya iya bambanta wanda ya ta'allaka ne da ikon ku na kaiwa ga masu ba da gudummawa.

Dandalin kamar su Kickstarter, Indiegogo, da kuma GoFundMe muhimmiyar hanya ne wa masu samar da kuɗin taron jama'a. Za ku iya wallafa bayanan akan kayayyakin ko sabis ɗin ku, tsara manufan tara kuɗi, da kuma iyakacin lokaci. Duk da haka, wasu dandalin ba sa sake kudaden idan ba a cimma burin ba sannan dandalin da a buƙata da kuma kuɗin ma'amala don katunan ajiyar kuɗi da na cin bashin kudi.



## Samarwan taron jama'a: Dandali

| Dandali | Amfani | Rashin amfani |
|---|---|---|
| KickStarter<br>www.kickstarter.com | • Dandalin bayar da lambar yabo waɗanda ke ba ku damar ba da tallafi ga magoya baya da abubuwan ƙarfafawa kamar kayayyaki da ragi<br>• Dandali samar da kuɗin taron jama'a da su ka fi sanuwa | • Za ku iya taɓa kuɗin ne kawai in kun cimma manufar ku<br>• 5% na Kuɗin dandali<br>• Biyan kuɗaɗen hada-hada (3%-5%) |
| GoFundMe<br>www.gofundme.com | • 0% na Kuɗin dandali<br>• Zaku iya rike duk gudummawa ko kun cimma manufar ku ko ba ku cimma ba<br>• Akwai taimakon gwanaye na 24/7 | • Kuɗaɗen hada-hadan katin ajiye kuɗi da katin cin bashi |
| Indiegogo<br>www.indiegogo.com | • Samun damar zaɓar tsayayyen manufa kuɗaɗe (manufofin duka ko babu) ko sassauƙan kuɗaɗe (zaku samu kuɗin ko kun cika manufar ku ko baku cika ba)<br>• Indiegogo InDemand zai ba ku damar ci gaba da tara kuɗi ko bayan lokacin neman kuɗaɗen na ku ya ƙare | • Suna karban cajar ku 5% na kuɗin dandali<br>• Biyan kuɗin aikin na wani dandali bayan su |

## Tallafi

Tallafi wani nau'i ne na tara kuɗaɗen da ake bayarwa ga kasuwanci don manufa fitacciya. Kuɗin za su iya fitowa daga ma'aikatar jama'a kamar hukumomin gwamnati, bankuna/ƙungiyoyin bashi, ko ba don riba ba.

Lokacin karbar bashi masu ba da bashin za su so ku nuna zaku iya biyan bashin, amma hukumar da ke ba da tallafi za su so kasuwancin ku yayi daidai da manufar su ko wani shiri na su na musamman. Saɓanin bashi, tallafi baya buƙatar biya kuma yawanci ba sa tasiri ga yanke shawara akan kasuwanci.

Wani fa'idar tallafin shine basu cika buƙatar tsayayyen bashi don ku cancanci shi. Duk da haka, tallafin sau da yawa suna da tsauraran hanyar duba cancanta waɗanda ke da wahalar cikawa, yanayin haraji, da kuma buƙatun yadda ake amfani da tallafin. Kamar yadda akasari su ke duba da yadda kasuwancin ku yayi daidai da manufa ko himmar su, masu sabon cike tallafn suna da matuƙar yawa ga kuma ƙarancin yiwuwar cin nasarar samun tallafin.



## Bashi

Lokacin da samar da kuɗi da kanku baya cikin zaɓin da kuke da shi, **Bashi** shine madadinsa. Bashin kuɗin don kasuwanci shine ya ke taimaka mu ku wajen kara Shigan kuɗi, siyan kayayyaki masu tsada, sannan kuma ya taimaka muku wajen haɓaka kasuwancin ku.

Ba kamar bashin kasuwanci na gargajiya ba, bashin ƙananun kasuwanci yawancin su ana bada sune akan kuɗin ruwa kaɗan, sauyayyun yanayin biyan bashi, da kuma sauƙin wajen cika bashin.

### Abubuwan da za ku yi la'akari da su lokacin yanke shawarar karɓar bashi:

- Amfani Kuɗaɗen
  - Masu bada bashi suna so suga yadda ku ka shirya yin amfani da kuɗaɗen, don haka kuyi mai kyau akan taka mai-main dalilin da ya sa kuke da buƙatar bashin
- Adadin Abun da za a Biya
  - Shin za ku iya samun adadin kuɗin da za ku biyan bashin na kowane watan da ku ka karba?
  - Shin za ku iya biyan bashin kuɗin ruwan ne kawai?
  - Ko za ku ajiye biyan bashin ku sai nan gaba in a ka buƙaci haka?
- Farashi
  - Ko za ku iya biyan kuɗin hidimdimur kuɗin ruwan?
  - Shin akwai wani kuɗin ne in an biya bashin da wuri?
- Lokaci
  - Lokacin da yafi dacewa ka name bashi shine lokacin da baka bukatar kuɗaɗen. Hanyar samun bashin yana ɗaukar tsawon lokaci, don haka yana da mahimmanci ku sani kafin lokacin



| Hanyoyin da za a Cika neman Bashi | |
|---|---|
| **Ku duba a gun masu baku Bashi** | • Farko, ku fara da ƙananun bankuna ko kungiyoyin bada bashi da kuke da dangantaka bashi da su. In banki ba tsaɓin ba ne, masu tallafawa na birni da kaga da kuma Cibiyoyin Ci gaban Kuɗi na Al'umma suma kyawawan madadin masu bada bashi ne |
| **Ƙayyade adadin Abun da za ku Nema Bashi** | • Ƙayyade adadin nawa ku ke da buƙata wajen biyan buƙatun kuɗin kasuwancin ku<br>• Ƙayyade in abinda za ku kashe na lokacin daya ne ko ya mai-maituwa |
| **Ku yi la'akari da sharruɗan mai bada bashi** | • Fahimci wannan irin takardu zaku buƙata don ku tura bukatar bashin |
| **Ƙayyade Manufa (Tayaya zaku yi Amfani da Kuɗaɗen)** | • Alar misali:<br>  ◦ Siyan sabin kayan aiki ko kayayyaki<br>  ◦ Siya ko kama hayan gida/gaban shago<br>  ◦ Biyan ma'aikata |
| **Lissafa adadin bashin da zaka biya** | • Ku tabbatar za ku iya samun abin da za ku biya kuɗin wata-wata na bashin kafin ku amince da karɓan bashin<br>• Ƙayyade yadda za ku biya bashin kuma idan kuna son lokacin biya yayi tsayi ko gajerta<br>• Tabbatar idan za ku iya canja adadin kuɗin da za ku dinga biya kowane wata ko kuma idan iri ɗaya ne kowane lokaci |

## Jerin abubuwan Cika Bashin Kananun Kasuwanci

Da zaran kun shirya cika bashi za ku buƙaci to shirya *takarđun kuđađen* da na *kasuwancn* ku don neman bashin.

**Takardun Kuđađen**

Zaku bukaci mafi na baya bayan nan

- Abubuwan haraji na kan-kan ku da na kasuwanci
- Bayanan kuđi ku ciki har da
  - Bayanin Riba da Asarar, takardar daidaiton kadarorin ku da bashi shuka ku, da bayanin zagayen kuđi
- Bayani a kan-kan ku wanda ya hađa da
  - Lambar zamantakewa ko lambar ITIN, kuđin shiga, tarihin bashi, tarihin cinikayya, da kuma biya da duba bayanan asusu

**Takarđun Kasuwanci**

- Tsarin kasuwanci da takarđun doka
  - Bayanan fara kasuwancin
  - Rigistan kasuwanci da kuma lasisi
  - Dokoki da kuma hanyoyin dokokin
  - Kwafi takardan hayar wajen kasuwancin ku idan kuna hayan waje ko hayar kowane irin kayan aiki mai mahimmanci ga kasuwancin ku
- Tsarin kasuwanci
  - Wanne ne damar a gare ku da za ku bayyana ma masu bada bashi akan kasuwanci ya cancanci saka hannun jari. Wannan zai hađa da hasashen kuđin ku, bayanin manufa, da dabarun ku.

**Don ƙarin bayani akan takarđun kuđi da na kasuwanci da ku ke buƙata don cika bashin dan Allah ko ziyarci: https://www.sba.gov/funding-programs/loans/7a-loans**

## NYS Cibiyoyin Ci gaban Kuɗi na Al'umma (CDFIs)

Cibiyoyin Ci gaban Kuɗi na Al'umma suna bada taimakon wa baƙi, matan da suka mallaka, da kuma al'umma masu matsakaicin kuɗin shiga ta hanyar bashi na karancin kuɗin ruwa, damammakin tallafi, da kuma ayyukan kudi kamar su koyarwa daya-da-daya da shirye-shiryen horar da masu buƙata.

CDFIs babbar fa'idace ba kawai don samar da kuɗi ba har don samun ilimi mai mahimmanci akan farawa, samar da kuɗi, da kuma haɓa ka ƙananun kasuwancin ku. A ƙasa akwai CDFI na tushen NYS waɗanda zasu iya tallafa muku akan tafiyar kasuwancin ku:

| | |
|---|---|
| **Accompany Capital**<br>Accompanycapital.org | **BOC Capital**<br>Boccapital.org |
| **Renaissance Economic Development Corporation**<br>renaissance-ny.org | **Bi**<br>https://pursuitlending.com/ |
| **TruFund Financial Services**<br>https://www.trufund.org/ | **Za ku iya jerin ƙarin bayan CDFIs a Jahar New York ta hanyar ziyarar**<br>https://www.nyscdfi.org/nyscdfis |